# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi
## Kashi na uku: Bashi na zubar da mutunci


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | James Muhando |
| Wanda ya fassara: | Danlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Mai ba da labari: | ɗan shekara 30 |
| Nana: | ’yar shekara 35 |
| Malama Rabi: | ’yar shekara 30 |
| Bash: | ɗan shekara 15 |
| Jamila: | ’yar shekara 15 |
| Ali: | ɗan shekara 15 |
| Ado: | ɗan shekara 45 |
| Adama: | ’yar shekara 19 |
| Hama: | ’yar shekara 19 |

**Mai ba da labari:**

Umhm! 'Yan'uwa, barkanmu da sake saduwa a kashi na uku na wannan shiri namu ta filin "Ji Ka Karu" mai suna "Aljannar kare – haɗarin afkawa cikin bashi". Ina fatan dai ba ku manta da ni ba: sunana Aliyu Bello. Riƙe matsayin mai kula da harkokin bashi a wannan banki na da ƙalubale irin nasa. Dole ne na rinƙa jurewa kuma na lura da irin abubuwan da mutane kan yi idan an hana su bashi, ko kuma an kai su ƙara saboda wani bashi da ba su biya ba! Amma dole ne a yi min uzuri, haka aikin ya gada. Yaya kuke jin zan yi idan irin su Kawu Natanko wanda muka ji labarinsa a wancan kashin ya zo wajena neman bashi? Kun dai tuna ai fitar da shi aka yi daga gidansa saboda bai biya kuɗin haya ba. Kuma na san ba ku manta da labarin abokin nan nawa ba, wato Bash, wanda ya daina zuwa makaranta saboda ya nemi kuɗi ya biya keken da ya ciwo bashi? Sai da ta kai yana ɓuya da daddare don kada ya haɗu da iyayensa!
Amma bari na ja ku mu koma zamanin ƙuruciyata yayin da nake Ali ɗina, ba Aliyu Bello jami'in kula da harkokin bashi ba. Mu fara daga gidan su Bash.

**Fitowa ta 1: A gidan su Bash**

**Malama Rabi:** Assalamu alaikum … Ina yini, Maman Bash?

**Nana:** Malama Rabi! Sannu da zuwa! Ke ce a gidan namu yau?

**Malama Rabi:** Na ga kamar kina wanke-wanke da sauri! Ko me ya sa?

**Nana:** Ai gara na yi maza na gama saboda na tatsi shanun nan kafin dare ya yi.

**Malama Rabi:** Ai kuwa gara ki hanzarta don kuwa ba zan bar gidan nan ba sai na sha shayi mai madara sosai!

**Nana:** To, zauna abinki!

**Malama Rabi:** To yaya Bash kuwa?

**Nana:** To kamata ya yi a ce kin fi ni sani, Malama Rabi, tun da ko da yaushe yana makaranta.

**Malama Rabi:** To yaya aka yi kuma ba na ganshi a makaranta tun da aka koma.

**Nana:** Me kike nufi?

**Malama Rabi:** Ni ma na ɗauka ko ba shi da lafiya ne, ko kuma wani abin dai ya same shi. Shi ya sa ma na zo!

**Nana:** Ai kullum sai ya tafi makaranta da safe. A'a! Ni fa ban gane ba.

**Malama Rabi:** Yau sati guda ke nan ban ga yaron nan a aji ba!

**Nana:** Da gaske kike, Malama? Yaron nan fa bai taɓa yi min ƙarya ba. Har ma ce min ya yi yana tsayawa a makaranta ya yi karatu, shi ne ya sa yake dawowa gida da daddare!

**Malama Rabi:** Ni ma dai abin ya ɗaure min kai, Maman Bash. Ni ma bai taɓa yi min ƙarya ba!

**Nana:** Ɗan halak! Ina kuma za ka, Bash? Zo nan! ... Daga ina kake? Tambayarka nake! Daga ina kake?

**Bash:** Makaranta.

**Nana:** Ina?

**Bash:** Makaranta.

**Malama Rabi:** Wace makarantar? Yau sati ɗaya ke nan ban sa ka a idona ba!

**Nana:** Ina kake tafiya kullum da safe da jaka sanye da 'uniform'? Ashe ban da yawo a cikin wannan garin ba abin da kake yi?! Bash! To ƙwace keken nan zan yi na kulle shi! Ina ma keken?

**Bash:** Yana wajen Jamila.

**Nana:** Wato komai naka rabar da shi kake yi ko? To maza je ka ka karɓo min keken nan yanzu-yanzun nan!

**Bash:** Ai ita ma tana hawa. Tare muka saya.

**Nana:** Ba abin da ya yi min zafi! Tafi ka karɓo mini shi yanzun nan!

**Mai ba da labari:**
To fa mutuncin Bash ya fara zubewa a gida da kuma makaranta. Karya yake cewa shi da Jamila suka mallaki keken nan. Gaskiyar magana ita ce, keken nan an yi masa fata-fata. To, ta yaya za mu kauce wa shiga irin wannan tsaka-mai-wuya? In ba ki da gashin wance, kada ki ce za ki yi kitson wance. In har ya zama lallai sai an ci bashi, to a yi wani kyakkyawan shiri! To amma fa ni ma sai daga baya na fahimci hakan tun da a halin yanzu ina aiki a banki. A wancan lokacin ni ma ba wai dabam nake ba.

**Fitowa ta 2 : Kogin Sabara**

**Jamila:** Bash, da ma bashi ka ciwo keken?

**Bash:** E, rabi kawai na biya na ɗauka. Sauran da ma zan biya ne satin da ya wuce. Amma ga shi na kasa biya saboda ban samu ba.

**Ali:** Kuma ga shi yanzu babu keken da kake ta haƙilon biya wa bashi ko?

**Bash:** E, ba shi ke nan ba!

**Jamila:** Kai, amma kana cikin matsala! Ta yaya ma ka samu har Iyabo ta ba ka bashin keke?

**Bash:** Kin san babana makanike ne, kuma abokin cinikin Iyabo ne. Mutum biyu daga abokan cinikinta kawai take ba wa bashi. Daga mijinta sai babana.

**Ali:** Wato baban naka ne ya karɓar maka bashin keken ke nan?

**Bash:** Uhmm… kusan hakan.

**Jamila:** Me kake nufi da kusan hakan? Irin wannan ƙumbiya-ƙumbiyar ce ta jefa ka cikin matsala!

**Ali:** Bi shi a hankali, Jamila! Bari ya yi bayani mana. … Me kake nufi ne, Bash?

**Bash:** Uhmmm, na rubuta wasiƙa ne na ɗan kwaikwayi sa hannun babana na nemi Iyabo ta ba ni bashin keken.

**Jamila:** Ka yi me?!

**Ali:** Lallai abokina, ka mutu!

**Jamila:** A ina ka sami kuɗin da ka biya rabin?

**Bash:** Shekara biyu ke nan ina tara kuɗi. Ba na so na koma makaranta ba ni da keke. Ni ma so nake na zama kamar sauran ɗalibai.

**Jamila:** To mu kuma mu mutu ke nan? Ba ka faɗa mana cewa kana satar sa hannun babanka ba, kuma kana karɓar bashin kayayyaki!

**Ali:** Kin ga, Jamila! Bash abokinmu ne, kuma abokai na haƙiƙa ba sa rabuwa ko mene ne ya faru. Dole ne mu san yanda za mu taimaka masa ya biya cikon kuɗin kafin a sani a gidansu.

**Jamila:** Ta yaya? A ina zamu samo Dala 60?

**Ali:** Yauwa! Na yi wani tunani! Ma iya cin bashi a wurin Malam Ado mai ba da bashi da ruwa!

**Jamila:** Me? Wannan tsohon mai laifin! Ba zai yiwu ba!

**Bash:** Malam Ado?

**Ali:** E mana, Malam Ado! Ba mugu ba ne kamar yadda kuke faɗa. Kawuna Natanko ya ranci kuɗi a wurinsa lokacin da ya zauna a nan.

**Jamila:** Wato maganar a ranto kuɗi kake yi ko? Ka manta maganar da muke yi ke nan? Cin bashi ne ya jefa Bash cikin matsalar da ya samu kansa a ciki fa!

**Ali:** To kina da wata shawara wadda ta fi wannan ne?

**Bash:** Muna fa ƙoƙarin warware wata matsala ne fa, Jamila. Na ɗauki alƙawari ba zan sake cin bashi ba!

**Jamila:** Alƙawari?

**Bash:** Kwarai da gaske, alƙawari.

**Jamila:** To shi ke nan. Za mu je wajen Malam Adon, amma daga wannan ba ƙari!

**Mai ba da labari:**
Nan take sai muka rankaya shagon mai ba da bashi da ruwa neman rance. A matsayinmu na farin shiga mun ɗauka karɓar irin wannan bashin abu ne mai sauƙi. Ai nan take muka gane kurenmu.

**Fitowa ta 3: A shagon mai ba da bashi**

**Ado:** Yauwa, Allah ya kama ka ne!

**Jamila:** Kai gayu, wallahi tallahi, mu kama gabanmu! Wannan mutumin ba shi da mutunci.

**Ali:** A'a Jamila, mu yi magana da shi tukuna mana.

**Ado:** Kada ka bari mu sake haɗuwa da kai ba tare da ka kawo min kuɗina ba! Mutumin banza mutumin wofi! … Ku fa yara, me kuke so?

**Bash/Jamila/Ali:** Sannu Malam Ado.

**Ado:** Na ce, me kuke so?

**Bash:** Muna so mu yi wata magana da kai ne.

**Ado:** Ku faɗa na ji! Kun tsaya haka sai ka ce tarin itace!

**Bash:** Muna buƙatar rance ne, Malam Ado.

**Ado:** Wane ne ke neman rancen? Ku?

**Ali:** E, mu ne muke buƙata!

**Ado:** Ba na ba wa ƙungiyar mutane rance. Wane ne yake so daga cikinku?

**Bash:** Ni ne.

**Ado:** Nawa?

**Ali:** Dala 60.

**Ado:** Ba da kai nake ba. Ko kai ne kake son rancen?

**Ali:** A'a!

**Ado:** To rufe mana baki! Nawa?

**Bash:** Dala 60.

**Ado:** To me za ka bayar na jingina?

**Bash:** Jingi...me?

**Ado:** Jingina mana. Kana tunanin zan ba ka rance ne ba tare da ka ba ni wata kadara ba?

**Jamila:** Malam Ado, mene ne jingina kuma?

**Ado:** Ba ki san jingina ba kike neman bashi? Fita daga nan! Sai kun zo mini da wata kadara da ya kai Dala 80 wanda zan dafe, har sai kun biya ni kuɗina. Ku ɓace min da gani mana!

**Fitowa ta 4: A kan hanyar dawowa daga shagon mai ba da bashi**

**Jamila:** Da ma na faɗa muku! Na san ba zai ba mu ko kwabo ba!

**Ali:** Ba fa cewa ya yi ba zai ba da kuɗi ba!

**Jamila:** To me ya raba dambe da faɗa? Ba zamu samu kuɗin nan ba.

**Bash:** Yanzu yaya zan yi ke nan?

**Ali:** To yanzu yaya za mu yi? Kuma maganar ita ce za mu kai wa Malam Ado kadara ko mene ne ma sunan abin yake ne?

**Jamila:** Kadara aka ce, kai Tundurƙi! Kai ba ka da ƙwaƙwalwa ne? Kadara ita ce abin da mutum yake ba wa mai bayar da bashi a matsayin abin da zai dogara da shi cewa za a biya shi kuɗinsa. Yawanci kuɗin kadarar yakan zarta ainihin kuɗin da mutum zai karɓa bashin. ... Ina za mu ne, Ali?

**Ali:** Ku dai ku biyo ni kawai!

**Mai ba da labari:**
A ɗaya ɓangaren kuma a cikin gari sai kawai Kawu Natanko ya yi taho-mu-gama da Hama. Ita maƙwabciyar Kawu Natanko ce a gidanmu na ƙauye, ta koma cikin gari ne don ta yi karatu. Kuma ma iya cewa ba sa shiri.

**Fitowa ta 5 : A cikin gari**

| | |
|---|---|
| **Adama:** | Kai! Amma da alama gidanku na ƙauye nan zai yi daɗin zuwa! Ya kamata wata rana mu je, ko Hama?! |
| **Hama:** | Haka ne, daga nan ma kya ga Kaka Dela. … Adama! Maza mu shige kantin can kafin wancan mutumin ya gan mu! |
| **Adama:** | Wane mutum? |
| **Hama:** | Wancan mutumin da ya sa kwat mana! |
| **Adama:** | Saboda me? Ba Kawu Natanko ba ne? |
| **Hama:** | Maza mu shiga! Na yi miki bayani daga baya! … Yauwa, na gode Allah! Ya shiga 'Jubilee Bank'. |
| **Adama:** | To, faɗa min, me ya sa ba kya son ku haɗu da kawunki? |
| **Hama:** | Ba kawuna ba ne! Kauyenmu ɗaya ne dai kawai da shi! |
| **Adama:** | Amma ai Kawu Natanko kike cewa da shi! |
| **Hama:** | Ai haka kowa yake ce masa! |

**Adama:** To me ya sa kika kauce masa?

**Hama:** Ai ɗan damfara ne! Ya gudo daga ƙauye ne saboda ya ci bashin mutane, kuma ba ya so ya biya su.

**Adama:** To, wai me ya sa kike gudunsa? Ai ba ya binki bashi ko?

**Hama:** Ai shi nake bi!

**Adama:** Ban gane na. Ai idan haka ne ma za ki fi son ku haɗu don ya biya ki kuɗinki!

**Hama:** Korarsa ma aka yi daga gidansa saboda ya kasa biyan kuɗin haya. Garari a titi kawai yake ta faman yi! Ba wanda yake hurɗa da shi saboda irin halayensa.

**Adama:** *Okay!* Wato kina gudun kar ya gan ki ya sake neman wasu kuɗaɗen daga wurinki ko?

**Hama:** Abin zai iya wuce haka ma. Zai iya ƙoƙarin shawo kaina da na amince masa ya zauna a gidana ma.

**Mai ba da labari:**
Yanzu kun fahimci abin da Kawu Natanko ya shirya zai yi a banki ko!
Idan kuna son sake sauraron wannan shiri, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kada ku manta, za ku iya saduwa da mu a shafinmu na 'Facebook'. Sai mun sadu, ku huta lafiya!